Darasi na 1

# Hawa Bisa—Gabatarwa



## A Duba a Takaice

### Manufa

Dalibai za su:

- kwatanta matakan girma a ruhu da hawa kan dutse;
- dauki littafin Yakubu a zaman jagora na hawa;
- san marubuci da manufar littafin Yakubu.

### Daga Maganar Allah

Yakubu 1:1
Zabura 121:1-8
1 Sarakuna 18:20-45
1 Sarakuna 19:1-3a,9-18

### Abin da kake Bukata

- Rubuta kowace kalma a kan takardar A—4 da manya harufa: TSABTA TSARKI ABOKANTAKA SANIN ALLAH SOSAI, SADARWA DA IYAYE, HIKIMAR ALLAH, IKON RAIRA YABO
- Domin Farawa; kananan itatuwa da babban kyalle mai duhu.

### Haddacewa

Zabura 121:1-2

## Farawa

TAMBAYA — *Ka taba hawan dutse?* (Malami, idan daliban suna rayuwa a inda babu dutse sai ka bayyana musu yanayi wurin da akwai duwatsu.)
ZABI yara biyar su gyara dutse ko tsanni da abubuwan da ka kawo. TAMBAYA — *Wadanne hatsarori ne mai hawan dutse zai fuskanta?* (Faduwa, tuntube, bata da sauransu.) *Wadanne ne ribar hawa saman dutse?* (Za a ji kai ma ka yi baban aiki, za a ga kyaun halitta na ke-waye daga sama.)
FADA — Rayuwar Kirista daidai yake da hawan dutse. Muna hawa zuwa sama kamar Yesu kuma muna girma cikin halin Kirista.
NUNA takardun da ka kawo ka kuma sa su a kewayen "dutse."
FADA — Wadannan su ne wasu kan ma-gana da za mu tattauna a shekaran nan. Yau za mu dubi wani nassi a Littafi Mai Tsarki da ya yi magana a kan dutse. Za mu fara koyo game da hawa bisa a tafi-yarmu ta ruhaniya.

## Gano Gaskiya

### Rukuni na 1

FADA wa dalibai su bude Zabura 121. Raira wakar da ta ambaci ayoyin nan idan kun sani.
FADA—Marubucin Zaburan nan mai yiwuwa yana hanyar zuwa Urushalima saboda yin bukin shekara na Yahudawa. Urushalima tana kan dutse. Mai yiwuwa matafiyin ya gaji ko ya ji tsoro yayin da yake tafiyar.
FADA masu su karanta ayoyin a zuci. Zabi wani ya karanta aya 2. *A ina maru-bucin ya ce taimakonsa yake fitowa? Yaya ya kwatanta Ubangiji?* (Mahaliccin sama da kasa.) *Ta yaya wannan zai zama ta'aziya ga mai hawa sama ta hanya mai wuya?* TAMBAYA—An ambaci kalman nan "makiyayi" ko "mai" lura sau kima a wannan zaburan. *A ganinka don me marubucin ya ambaci kalmomin nan?*
FADA wa kowane dalibi ya karanta aya 3 -8 tare da dalibin da ke kusa da shi don ya san abin da Allah ya alkawarta. Bayan haka sai su bayyana amsoshinsu. KARANTA aya 1-2. RUBUTA maganar nan a kan allo: A **LOKACIN DA KAKE HAWA, KA TUNA CEWA KAUNAR ALLAH DA KULARSA SUNA KANKA.**
Tuna masu cewa muna tunanin rayuwar Kirista kamar hawa. Muna hawa zuwa girma a hali na Kirista.

### Part 2

TAMBAYA—*Wane littafi ne a Sabon Alkawari yake dauke da shawara domin yin rayuwa irin na Kirista?* (Littafin Ya-kubu ne.) Za mu dauki wannan littafi a zaman jagora wanda Allah ya bamu don ya taimake a hawanmu zuwa girma a halinmu na Kirista. Wasu darusanmu na wannan shekara za mu yi nazari ne a Yakubu. KARANTA Yakubu 1:1 ka kuma RUBUTA bayani game da littafin Yakubu a kan allo. Marubuci —Yakubu, dan'uwan Yesu.
FADA—Da fari Yakubu bai yarda cewa Yesu Dan Allah ba. Daga baya ba kawai Yakubu ya zama mabiyin Yesu ba, amma ya zama shugaban ikilisiya a Urushalima. Wadanda aka rubuta musu—Kirista Yahudawa da ke warwatse saboda tsanani. Dalilin rubutun—Ya koyar da kuma karfafa mutanen da ke warwatse suna shan wahala.

## Kalubala

FADA—**Shafin Matashi** na yau yana tuna mana labari daga Littafi Mai Tsarki da ya ambaci dutse. Fada wa dalibai su **Cika shafin Matashi** ko su yi a gida.
FADA—Za mu iya fuskantar wahaloli yayin da muna hawa zuwa yin girma a rayuwarmu. Sanin cewa karfi da kaunar Allah suna kanmu, na iya karfafa mu a hawanmu. Ka KALUBALANCI dalibai su haddace Zabura 121. ZABI dalibi ya karanta **Kwayar Magana**.

# Darasi na 1

## Hawa Bisa—Gabatarwa



**A 1 Sarakuna 18-19, Iliya ya "hau dutse." Karanta maganganu na biye. Yi tunani a kan amsar tambaya na 4. Ka shirya saboda tat-taunawa a aji.**

Sayawa da karfi

**Zabura 121:1-2**

Na duba wajen duwatsu, Daga ina taimakona zai zo? Taimakona zai zo daga wurin Ubangiji, wanda ya yi sama da kasa.

1. Hawa na fari na Iliya kan dutsen Karmel (1 Sarakuna 18:20-40). Allah ya mori Iliya ya nuna wa mutananen Israila ikonsa a kan anna-bawan karya. Tana yiwuwa Iliya ya yi farin ciki a "hawan dutsensa na fari."

2. Hawa na biyu na Iliya kan dutsen Karmel (1 Sarakuna 18:41-45). Da Allah ya amsa addu'ar Iliya, sai ya aiko da ruwan sama bayan an yi rashin ruwa (fari) na shekara 3. Iliya mai yiwuwa ya karfafu da ganin ikon Allah, bayan Allah ya sauko da ruwa.

3. Hawan Iliya a Dutsen Horeb . Karanta 1 Sarakuna 19:1-3a, 9-18. don me Iliya ya ji tsoro? Wane dalili ne Iliya ya fada wa Allah kan buyarsa a kogo a bisa Dutsen Horeb? Ta wane yanayi ne Allah ya yiwa Iliya magana? Wace karafafawa ce Allah ya yi wa Iliya a aya 18?

4. Hawan dutsenka. Wadanne wahaloli ne kake samu a yayin da kana hawa sama zuwa yin girma a halinka na Kirista da kuma zama kamar Yesu? Wane abu ne zai taimake ka a wadannan wahaloli?

### Kwayar Magana

Rayuwar Kirista tana kama da hawan dutse. Muna hawa sama don mu zama kamar Yesu da yin girma a halinmu. Allah yana kula da mu a kowane lokaci yayin da muna hawa. Littafin Yakubu ya bamu shawarar da za mu bi don ya taimake mu a hawanmu.